**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**

A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)

**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.14 **Website:** www.ssu.edu.ng |**Issue 1** | **April 2025**|

# Gurbin Musulunci A Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Hassan Muhammad**

Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Jihar Sakkwato

**Corresponding Author: Hassan Muhammad** muhammadhassan6060@gmail.com

07037158242

**Tsakure** ***Tsakure***

*Mawaƙan Hausa mutane ne da Allah ya yi wa baiwa da basira da hikimomi wajen tsara zantuttukan hikima a cikin baitocin waƙa ko ɗiyan waƙa. Wannan baiwa da Allah ya yi musu ya sa ake tsintar abubuwa nagartattu da yawa waɗanda suka shafi hanyoyin rayuwar al'umma a cikin waƙoƙinsu. Da ma shi harshe sha-kundum ne a rayuwar kowace al'umma domin shi ke bayyana kowane irin al'amari da zai fito cikin al'umma musamman fasahohinsu na baka. A dalilin haka ne aka shirya wannan maƙala da aka yi wa take da Gurbin Musulunci a wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi. Wannan maƙala ta ƙudiri fito da wasu abubuwa da Kassu Zurmi ya ambata a cikin ɗiyan wasu waƙoƙinsa da ya yi, waɗanda nazari ya gano cewa ko shakka babu abubuwan an ambace su ne a dalilin tasirin da addinin Musulunci ya yi a rayuwar mawaƙin. An zaɓi waƙoƙi biyu daga cikin waƙoƙin da mawaƙin ya yi domin fito da ƙudirin maƙalar. Waƙoƙin su ne 'Waƙar Iro Shayi ɗan gidan Labbo' da 'Waƙar Malam Sanda ɗan Ruhwa'i'.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Wannan takarda ta yi ƙudirin bayyana gurbin Musulunci a wasu daga cikin waƙoƙin Kassu Zurmi wanda yake makaɗin maza ne. Takardar za ta yi ƙoƙarin fito da bayanai kan wasu abubuwa da aka ci karo da su a ɗiyan waƙoƙin makaɗin waɗanda aka tabbatar da tasirin Musulunci ne ya sa aka ambace su. Kafin nan takarda za ta fara da kawo bayanai kan taƙaitaccen tarihin Makaɗa Kassu Zurmi da bayani taƙaitacce kan fitilun kalmomi kamar kalmar adabi da kalmar gargajiya da kalmar gurbi da kalmar Musulunci. Daga nan sai a yi bayanin kan ɗiyan waƙa waɗanda ake ganin akwai tasirin addinin Musulunci cikin su. A ƙarshen aikin za a zo da sakamakon bincike.

## 1.1 Hanyoyin Tattara Bayanai

Da ma shi bincike na ilimi kowane iri ne, kafin a aiwatar da shi yana buƙatar a bi wasu hanyoyi da za a samu ingantattun bayanai waɗanda za su taimaka wajen kafa hujja ga binciken. A wannan bincike an bi wasu hanyoyi domin samun cikar manufar inganta shi waɗanda suka haɗa da:

i. Binciken kafar sadarwa domin zaƙulo waƙoƙin Kassu Zurmi daga manhajar bidmit (vidmate) da sauraronsu don fito da abin da nazari ke buƙata.
ii. Samo matanin rubutattun waƙoƙin makaɗin don tantance kalmomi da jumlolin da makaɗin ya faɗa.
iii. Tattaunawa da masana adabin Hausa daban-daban da kuma waɗanda suka naƙalci waƙoƙin makaɗin kamar Abubakar Sayaya da Abdullahi Birnin Magaji da Ɗanmadamin Birnin Magaji da sauransu da kuma karanta rubuce-rubucen da aka yi a kan makaɗin.

## 1.2 Taƙaitaccen Tarihin Kassu Zurmi

Alhaji Abubakar Kassu Zurmi shi ne cikakken sunansa, an haife shi a garin Magarya da ke cikin ƙasar Zurmi wadda ita Zurmi ƙaramar hukuma ce ta jihar Zamfara. Kassu Zurmi ya zauna ne a Kadawa wanda yake gari ne da nisansa kafin a ƙarasa Magarya tafiyar kilo mita biyu ne. Sunan mahaifin Kassu Zurmi Muhammadu Ganga wanda yake makaɗin farauta ne kuma a wurinsa ne Kassu ya yi gadon kiɗan farauta. Kassu bai yi ilimin zamani ba amma ya ɗan taɓa karatun Alƙur'ani, kuma tun lokacin da ya isa a kira shi da mutum mai hankali ya fara bin mahaifinsa wurin kiɗan farauta (Magaji, 2016:9).

Duk wanda ya san Kassu, ya san shi ne a matsayin makaɗin maza wato dukkan waɗanda yake yi wa kiɗa jarumai ne waɗanda ko a cikin maza lalle sun yi zara wati sai jarumin da zai iya bari a yanke shi ko a sare shi, ko jarumin da zai iya shiga cikin ruƙuƙin daji domin farauta da jarumin da zai iya bin dare ya tafi har wani gari domin ya yo sata. Haka kuma a matsayinsa na makaɗin farauta ba wai gidajensu kawai yake bi idan suna biki ya kama ba, a'a tare da shi ake zuwa dajin farautar (Magaji, 2016:10). A cikin waƙar Gagarau na Magaji cewa ya yi:

Jagora: Tahiya Madoka ko dajin Kuna,
Kowaj ji 'yan kalangaina na tahi an nan,
Sai ɗa da ɗa ka kai naman daji.

Kassu yana da makaɗa guda uku, kowane daga cikin su yana da kalangunsa wanda a koyaushe idan ban da wurin farauta suna tare. Wani muhimmin abu shi ne duk makaɗansa iyakacinsu kiɗan, Kassu ne yake tsara waƙoƙinsa kuma shi kaɗai yake yi, ba a yi masa amshi, don haka Kassu makaɗi ne na kaɗaita wanda yake ƙulla waƙa shi kaɗai, ba tare da an yi masa ƙari ko amshi na gindin waƙa ba (Magaji, 2016:13).

Kassu ya sami ɗaukaka a wajen kiɗan farauta da na tauri, har ma da na ɓarayin wanda hakan ya sa Sarkin Zurmi ya naɗa shi sarkin makaɗan maza na ƙasarsa. Kassu ya yi arziki a kan wannan sana'a ta kiɗa duk ko da yake yana haɗa wa da noma amma kiɗan shi ne a gaba. Bayan haka Kassu yana da kyakkyawar dangantaka tsakaninsa da sauran makaɗan ƙasar Hausa kamar Alhaji Mamman Shata wanda har biya masa kuɗin jirgi ya yi ya je Makka ya yiwo sallah kamar yadda ya nuna a wani ɗan waƙarsa:

Jagora: Kai ubangidan Shanu da Gambu,
Na Dela albarkacinka nis sabu da Shata,
Hay yay yi man kujerah haji niz zo.

Magaji (2016:10) ya bayyana cewa waƙoƙi biyu ne na 'yan tauri suka fito da Kassu Zurmi sarari har aka san shi, kuma waƙoƙin suna cikin tsofaffin waƙoƙinsa da aka saka a garmaho. Waƙoƙin su ne 'Waƙar Nomau Namagarya da 'Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo. Haka ya sake bayyana cewa kafin rasuwar Kassu Zurmi ya yi fiye da shekaru ashirin bai je farauta ba, a dalilin gwamnati ta hana saboda wasu dalilai wanda daga cikin su akwai yawan rasa rayuka da ake yi in an fita.

**1.3 Adabi**

Da ma abin da masana suka kira da adabi shi ne, fasahohi da hikimomin rayuwar al'umma da ke ƙunshe cikin harshensu, musamman abubuwan da suka ƙirƙira ta hanyar tunanin da yake ɗarsuwa a tsare-tsaren rayuwarsu. Su waɗannan tsare-tsaren rayuwarsu sun ƙunshi zantuttukansu na azanci masu saka nishaɗi kamar waƙoƙinsu na baka da irin kirari da take da salon magana da gajerun labaransu na gargajiya da sauransu da yawa. Haka su waɗannan abubuwa sun ƙunshi nau'o'in azancin harshe kamar karin magana da baƙar magana da adon harshe da ire-irensu cikin abubuwan da ke ƙawata magana da nuna ƙwarewa cikin harshe (Garba, 2020:184).

Idan aka juyo kuma a mahangar zamani wasu masana sun nuna ma'anar adabi ta wuce ƙirƙirarrun zantuka da rubuce-rubucen al'umma, ta kai har ga dukkan nau'o'in rubuce-rubuce na ɓangarori daban-daban kamar ɓangaren falsafa da na tarihi da na kimiyya da na harshen Hausa da Larabci da na fannonin gona da abubuwan da suka shafi Musulunci, waɗanda suke tattare da wani tsari da salo da tasirin a kan masu karatu ko masu sauraro (Abrams da Harpham, 2012:199-200). Haka kuma a wannan mahangar ce dukkan rubuce-rubucen da suka shafi addinin Musulunci ake kira su da adabin Musulunci. A ƙarƙashin wannan ma'anar ce kuma ake danganta kalmar adabi ga Alƙur'ani da hadisi, wato rubuce-rubuce na musamman a kan Musulunci domin al'ummar Musulmi. Haka kuma kalmar adabi tana ɗaukar manufar rubuce-rubucen wani marubuci kamar Abubakar Imam sai a ce Adabin Abubkar Imam ko na Ɗangambo da sauransu (Garba, 2020:185).

**1.4 Gargajiya**

Bargery (1993:366) da Awde (1996:51) da CNCN (2006:159) sun bayyana cewa kalmar gargajiya na nufin shuɗaɗɗen zamani ko al'ada ko wata ɗabi'a ko kuma wani kaya na zamanin dauri, sai suka ƙara da cewa idan aka ce wannan na gargajiya ne to ana nufin abin da aka gaje shi ne kaka-da-kakanni. A taƙaice tana nufin irin tanade-tanaden da Hausawa suka yi wa kansu domin tafiyar da rayuwarsu tun can asali, ba tare da dogaro da wata al'umma ba. Wannan ya haɗa da hanyar bauta da ta neman abinci da ta neman waraka da sauran tsare-tsare da tanade-tanaden rayuwa. Maguzanci shi ne tsarin rayuwar Bahaushe na asali, wanda kuma cikakkiyar hanyar rayuwa ce mai daɗaɗɗun al'adu ingantattu, wadda a kodayaushe take ƙoƙarin watsar da munana a rayuwar al'umma Hausawa a gargajiyance, ta hanyar tsafi da camfi da ƙirƙire-ƙirƙire domin tafiyar da rayuwa mai inganci (Gusau, 2008:19).

**1.5 Musulunci**

Musulunci shi ne addinin da musulmi suke bi na bauta wa Allah shi kaɗai babu tarayya da shi, kuma Annabi Muhammad Manzonsa ne (Sa'id, 2006:353). Masana irin su Wudil (1989:14-16) da Ibrahim (1989:32-40) da Yahaya (1988:8-13) da Abba da wasu

(2017:xi) dukkansu sun ƙarfafa cewa Hausawa sun fara hulɗa da Larabawa tun a ƙarni na shida kuma hulɗar ta yi ƙarfi ƙwarai a ƙarni na tara zuwa na goma sha biyu a dalilin fataucin ratsin sahara watau *Trans-Saharan Trade* da kiraye-kirayen na da'awar yaɗa addinin Musulunci.

Musulunci yana da matuƙar muhimmancin cikin adabin Hausa domin ya shafi nau'o'in salon rubuce-rubuce da saƙonni da ake isarwa cikin wannan adabin. Da ma shi Musulunci hanya ce wacce take ƙunshe da dukkan tsare-tsare da tanade-tanaden rayuwar ɗan adam tun daga farkon rayuwa har zuwa ƙarshenta. Watau daga farkon duniya zuwa ƙarshenta, domin dukkan Annabawan da Allah ya aiko duniya, hanyar Musulunci ita ce hanyar da suka rayu kuma suka shiryar da dukkan al'ummar duniya zuwa gare ta (Albarbahari, 2013:16). A taƙaice ana iya cewa Musulunci ginshiƙi ne mai cikakken ƙarfi da iko da ke ƙarfafa ɗabi'a da hikima da ilimi a cikin adabin Hausa, tare da saka ƙima da daidaito ga rubuce-rubucen na ɓangarorin adabi musamman kan abin da ya shafi waƙoƙin baka da rubutattu da ƙagaggun labarai da wasannin kwaikwayo.

### 1.6 Gurbi

Kalmar gurbi kamar yadda Sa'id (2006:176) ya bayyana ita ce rami marar zurfi a ƙasa, haka tana ɗaukar ma'anar hali ko muƙami ko matsayi da aka keɓe don ba da aiki. A harshen Hausa kalmar gurbi tana da ma'ana mai dangantaka da matsayi ko muƙami, musamman a cikin tsarin shugabanci ko zamantakewa. Kenan ana iya kallon kalmar gurbi a mtsayin wuri ko kujera ta musamman da mutum ke da ita a wani matsayi da aka ba shi ko aka naɗa shi, musamman sarauta ko shugubanci.

### 2.0 Gurbin Musulunci a wasu Ɗiyan Waƙoƙin Kassu Zurmi

A yanzu kuma kai tsaye wannan nazarin zai fara bayani a kan wasu ɗiyan waƙoƙi da Makaɗa Kassu Zurmi ya ambata waɗanda ake ganin lallai tasirin Musulunci ne ya gina su. Ga su kamar haka:

Jagora: Maza malan Ɗan'ruhwa'i mai daga,
Kun ji kiɗin malan wanda ba a so nai,
Jama'a malamai iri-iri ne,
Waɗancan namu ba na nan ba,
Koko han nan akwai mutane nai.

Jagora: Na san Malan Sanda ba ya son sallah,
Kana ba ya son kono,
Kuma bai ya da hidda zakka,
Ɗan'ruhwa'i mai daga,
Ai malam duw wada ba a so ka yi,
Ɗan'ruhwa'i mai daga.

A waɗannan ɗiyan waƙoƙin da ke sama Kassu Zurmi ya ambaci wasu abubuwa waɗanda suke da alaƙa da Musulunci, kamar malami da ya ambata ya ce malamai iri-iri ne, amma kuma ya nuna akwai kiɗin malan wanda ba a so, haka akwai malamai irin nasu waɗanda ke zama tare da su akwai waɗanda ba sa zama tare da su waɗanda kuma su ne malaman gaskiya, sannan ya ambaci sallah da kono da zakka.

Babu shakka duk wanda aka kira da malami a mahanga ta addinin Musulunci to jama'a suna yi masa kallon babban mutum mai matsayi cikin al'umma. Sai dai kuma kamar yadda

Kassu ya ambata cewa su malaman iri-iri ne, to lallai abin haka yake, domin a cikin kowace al'umma musamman Hausawa, akwai malamai kala-kala, don haka ne ma suka kasa su gida-gida, misali akwai malamai waɗanda suka cancanci a kira su da malamai saboda zurfin ilminsu na addini kuma su ne masu koyar da al'umma yadda ake bautar Ubangiji da yadda ake kiyaye dokokinsa da sauran abubuwan da ke sa a samu tsira daga azabarsa a ranar alƙiyama. Haka akwai malaman da ba su cancanci a kira su da malamai ba, saboda ƙarancin ilminsu, don haka ne ma masu hikima ke cewa 'ƙaramin sani ƙuƙumi'. Ga wasu ire-iren malaman addini a Musulunci:

i. Malamai na Alƙur'ani: Su ne masu koyar da karatun Alƙur'ani tare da tajwidi
ii. Malamai na Fiƙhu: Su ne masu koyar da dokokin shari'a da ibada.
iii. Mufassirai: Su ne– masu fassara Alƙur'ani.
iv. Muhaddisi: Su ne masu koyar da hadisai na Annabin rahma
v. Ulama: Su ne manyan malamai da suke da ilimin addini mai zurfi.
vi. Shehu/Sheikh: Su ne galibi shugabannin addini ko shugabannin ɗariku kamar Tijjaniyya ko Ƙadiriyya.
vii. Imam: Shi ne wanda ke jagorantar sallah ko al'umma
viii. Khalifa: Shi ne wakilin jagora, musamman a tsarin ɗariƙa.
ix. Malamai na Ɗariƙa: Su ne masu koyar da tarbiyya da ilimin tasawwuf wato ilimin zuciya da ruhaniyya. Haka akwai Izala waɗanda suka fi kiran kansu da Ahlussunna, kuma suna kallon wasu ayyukan da malaman ɗariƙa ke aiwatarwa bidi'a ne.[1]

Ta la'akari da wannan ɗan bayanin da aka yi na ire-iren malamai, za a ga duk cikin waɗannan malamai da aka ambata, ba su ne Kassu ke nufi ba, saboda ya nuna cewa Malan Sanda ba ya son sallah, ba ya son kono kuma ba ya fitar da zakka. Waɗannan abubuwa da Kassu ya ce Malan Sanda ba ya so, abubuwa ne masu ƙarfin gaske a Musulunci. Kenan lalle Malan Sanda ba ya cikin irin malaman da ya kamata a yi koyi da su.

Jagora: Watan azumi ya kama,
Ana ta horon jahilawa,
Naz zo ga Malan Ango wannan,
Wanda an na Allah,
Na ce Ango hwaɗa mana,
Ka san wanda am maras sani jaki,
Watan azumi ya kama,
A mu kai mu ƙaru.

Jagora: Ya ce madalla tambaya daidai,
Ku rage alhwasha,
Ku bar batutuwan banza,
Watan Labarana hwa ba ya son wargi,
To in kau ya mutu,
Zakka ku kai kun kono,
Wad da kowa ka gyara gonai nai,
In ji wa nai hwa.

[1]Tattaunawa da Malam Isma'il Sani Midiri ɗan shekaru 48 a harabar makarantarsa da ke Unguwar Minannata Sakkwato ranar Alhamis 27/03/2025 da misalin ƙarfe biyar na yamma.

A waɗannan ɗiyan waƙa da ke sama Kassu ya nuna muhimmancin azumi, inda ya nuna idan watan azumi ya kama, za a riƙa horon waɗanda a jahilai cewa su kama ayyuka na ƙwarai su bar duk wani abu da zai iya ɓata musu azumi. To a wannan lokaci na azumi ne Kassu ya je wajen Malan Ango ya tambaye shi abin da ya kamata mutun ya yi don ya tsira da ladar azuminsa, don shi wanda a jahili maras ilimi daidai yake da jaki. Shi kuma Malan Ango ya ce masa cikin abubuwan da ba a so a yi akwai alfasha da batutuwan banza, don shi watan Ramadana wata ne na samun rahama da gafara da ɗiyauci daga wuta, ko kaɗan ba a son a yi wargi cikinsa. Haka idan an kammala shi akwai zakkar kono da ake fitarwa wadda bayaninta ya gabata a ɗiyan waƙar da suka gabaci waɗannan.
Yanzu kuma za a zo da taƙaitaccen bayani game da abin da Musulunci ya yi magana a kai, a kan waɗannan abubuwa da Kassu ya faɗa a ɗiyan waƙarsa, wato sallah da azumi da zakka da kono.

A Musulunci sallah da azumi da zakkah dole ne ga kowane musulmi baligi mai hankali, suna daga cikin shika-shikan Musulunci guda biyar, sai dai ita zakka ba ta wajaba a kan kowa ba sai wanda dukiyarsa ta kai wani gwargwado wanda shari'a ta tanada, wannan gwargwadon shi ake kira da *nisabi*. Kono kuwa, wata zakka ce da ake fitarwa bayan an kammala ibadar azumin watan Ramadana.

Sallah ibada ce da ake yi sau biyar a rana da dare, cikin tsari na musamman. Matsayinta kuwa, ita ce ginshiƙi na biyu bayan shahada. Wajibi ce a kan kowane musulmi baligi mai hankali. Wanda ya ƙi yin sallah da ganganci, malamai da dama sun kira hakan da kafirci. Muhimmancinta yana da yawa kaɗan daga ciki shi ne, hanya ce ta samun kusanci ga Maɗaukakin Sarki, haka tana wanke zunubai, sannan kuma, ita ce farkon abin da za a fara tambayar bawa game da ita cikin ayyukansa a ranar alƙiyama. Saboda matsayin sallah, lokacin da za a wajabtata ga bayi, ba wahayi aka yi wa fiyayyen halitta ba, a'a sai da aka yi tafiyar dare da shi daga Makka zuwa Baitil Maƙdasi (*Isra'i*) sannan daga nan aka hau da shi zuwa sama domin ganawa da Ubangijinsa (*Mi'iraji*) wanda a can ne ya karɓo ta.[2]

Azumi kuwa shi ne, barin abinci da abin sha da hulɗar aure daga alfijir har zuwa faduwar rana, a cikin watan Ramadana. Matsayinsa kuwa, shi ne na uku a shika-shikan Musulunci. Wajibi ne a kan kowanne musulmi baligi, mai lafiya, wanda ba ya cikin tafiya ko wani hali na musamman kamar ciwon da ke buƙatar sauƙi. Muhimmancinsa kuwa, shi ne yana koyar da ɗa'a da tsoron Allah. A tare da shi akwai lada mai girma. Haka yana wanke zunubai da kuma ɗaga daraja a wurin Allah.[3]

Zakka na nufin wani kashi na dukiyar Musulmi da ya kai wani matsayi, da ake cirewa a shekara domin ba wa waɗanda suka cancanta kamar yadda Allah (SWT) ya tsara a cikin Alƙur'ani da hadisan Annabi Muhammad (SAW). Zakka farilla ce ga kowanne musulmi mai dukiya wato dukiyar da ta kai *nisab* (matsakaicin adadin dukiya da ake buƙata kafin zakka ta zama wajibi). Da ma ita kalmar zakka tana nufin tsafta da albarka. Ana ɗaukarta a matsayin hanya ta tsarkake dukiya daga haram da ƙeta da hasada da zuciyar kama-karya. Zakka na taimakawa wajen rage bambanci tsakanin masu arziki da matalauta, ta

[2] Don tabbatar da ingancin wannan magana da aka ambata a dubi littafin *Sahihul Buhari*, hadisi mai namba 342 a babin da aka yi wa take da 'Yadda aka wajabta sallah a lokacin da aka yi *Isra'i*', haka a dubi hadisi mai namba 413 a cikin littafin *Sunan Attirmizi*.
[3] A dubi *Alƙur'ani* Sura ta biyu aya ta 183 da littafin *Sahihul Buhari*, hadisi mai namba 1792 a babin wajabcin azumin watan Ramadana da hadisi mai namba 1804 a babin da aka yi wa suna da 'Wanda bai bar ƙarya ba da aiki da ita a cikin azumi'.

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

hanyar raba arziki cikin adalci. Ita wannan zakka nau'i biyu ce, akwai zakka kan dukiya game da abin da ya shafi zinariya da azurfa da kuɗi da amfanin gona da dabbobi da kasuwanci. Bayan ita akwai zakkar fidda-kai da ake bayarwa a ƙarshen watan Ramadana kafin sallar idi wadda ake kira kono, bayaninta zai zo a gaba. Laifi ne babba ga wanda ya ƙi bayar da zakka da gangan bayan ta wajaba gare shi. A wasu lokuta, idan gwamnati ce take mulki da shari'a, ana iya tilasta shi ya biya. A lahira, Allah zai azabtar da waɗanda suka ƙi bayar da zakka kamar yadda ya zo a hadisi da ayoyin Alƙur'ani.[4]

Kono kuwa shi ne ake kira da *Zakatul-Fitr* a Larabce. Haka ana kiransa da zakkar fidda-kai a harshen Hausa. Ita wannan zakkar ta fidda-kai wata nau'i ce ta zakka da ke da hukunci na musamman a Musulunci. Amfaninta shi ne, tsaftace azumi daga kurakurai da taimakawa miskinai su sami abinci ranar idi. Haka hanya ce ta haɗa kan-juna a cikin al'umma da kuma nuna an kammala azumin Ramadana da kyakkyawan aiki. Wani abu da ta ƙunsa shi ne, duk musulmi, ko mace ko namiji, ko yaro ko babba ana fitar masa da ita matsawar ya kasance akwai abinci fiye da buƙata da iyalai za su ci a ranar idi da daren idi. Uba ko mai riƙe da nauyin jama'a yana ba da zakkar kan yara ko waɗanda ke ƙarƙashinsa. A taƙaice dai zakkar fidda-kai hukuncinta wajibi ne. Ana fitar da ita don tsaftace azumi da taimakawa mabuƙata. Wanda ya bar fitar da ita cikin ganganci yana cikin saɓo, kuma ya rasa lada mai girma. Wannan wata dama ce ta nuna alheri da tausayi a cikin Musulunci.[5]

Jagora: Sai Malan Sanda ya aboce mai,
Wai ni wane horon wa?
Yac ce kai kui ta wanda kun ka iya,
Ango yana nan da jaye-jaye nai.

Jagora: To ni kau da ban barin bashi,
Nac ce to Sanda ba ni horo,
In ka walwale horon wanka,
Hwaɗa ma ni,
Ka san maras sani jaki,
A'a mu kai mu ƙaru.

Jagora: Yac to duw wanda an ka wa hujja,
Dan Allah shi auri mace biyu,
Mai yag guda ka jin tsoro dai,
Ba su ba ka al lasa ba,
Buzu-buzu da ranka da riga,
Ɗan Na'iro hag ga tsoho nai,
Da shi ak shige da dangi nai.

A waɗannan ɗiyan waƙa ci gaba da bayani ne Kassu ya yi a kan horn da ya ce ana yi wa jahilai da su daina alfasha da wasu miyagun ayyukka idan watan azumi ya kama. Ya nuna cewa shi Malam Ango da ke wannan horo jaye-jaye ne kawai yake yi, kowa ma ya je ya ci gaba da abin da ya ga dama. Bayan haka, Kassu ya nuna shi fa Malam Sanda shi ne nasa, kuma a wurinsa ne kawai zai iya karɓar umurni. Kenan wannan zai nuna cewa horon Malam Ango da ya fara yi a farko, to kamar an ɗan sosa zuciyar Kassu don bai so haka ba,

[4] Duba *Sahihul Buhari* a babin wajabcin zakka hadisi mai namba 1331.
[5] Duba *Sahihul Buhari* a babin wajabcin zakka hadisi mai namba 1432.

wannan ne ma ya sa ya ce bai barin bashi. A taƙaice dai horon da Kassu ya ce Sanda ya yi masa na biyan bashi ne.

Wani abin lura da za a yi duba da shi a ɗiyan waƙar wanda ƙarara akwai tasirin Musulunci a ciki, shi ne inda Kassu ya nuna cewa shi fa maras sani jaki ne, don haka su a ba su horo don su amfani da ilimi. A wannan gaɓar binciken zai iya kafa hujja da faɗar Allah Maɗaukakin Sarki a Sura ta 39 aya ta 9 a cikin Alƙur'ani mai girma inda ya ce "Ka ce musu ya kai Manzo shin waɗanda suka sani suna daidai da waɗanda ba su sani ba", amsa a nan ita ce, ba su zama daidai. A wani wurin cikin *Alƙur'ani* (Sura ta 62 aya ta 5) Ubangiji ya ba da misali da ɗaya daga cikin waɗanda aka ba wa littafi su ne Yahudu da aka ce su yi aiki da littafin da aka aiko Annabi Musa da shi zuwa gare su wato *Attaura*, amma sai suka ƙi, sai Ubangiji ya misalta su da jaki wato su daidai suke da jaki wanda aka ɗoro wa littattafai kamar irinsu *Attaura* da *Injila* da *Zabura* da *Alƙur'ani*, wanda ga shi ɗauke da littattafan amma bai san komi ya ɗauko ba, balle ma har ya san ilmummukan da ke cikinsu.

Ɗiyan waƙa na gaba da za a yi magana masu ɗauke da tasirin Musulunci su ne waɗanda Kassu ya nuna matsayin amanar Allah a cikin waƙar Shayaya ɗan gidan Labbo.
Ga yadda ɗiyan waƙar suka zo:

Jagora: Katakoron Lando Iro Na Ummaru kura mai guzurin kunya,
Sai da za mu watcikkewa kana uwayen matan ga sun ka jawo ni,
Gani ga 'yan matan ga ga uwayensu mu kaɗai cikin zaure,
Kassu amanar Allah ka ba mu labari,
Nic ce wane labari?
Labarin Shayi ɗan gidan Labbo,
'Yan mata sun walwale baikonsu,
Sun ce Shayaya za shi rankon su,
To shi muka son ka ba mu labari in akwai gidan kirki,
Nic ce yau kau dattiɓe kun ɗamarshe ni,
Ya hi ku koma ku sake ɗan shaida
Na Abu ɗan uwana ne,
Mutun kau bai shaidaɗ ɗan uwansu ko hwada.

Jagora: Kassu amanar Allah ka ba mu labari,
Ni kau amanar Allahg ga ɗai ka sha min kai,
In na bi amanar Allahg ga na yi ɓatanci,
Kuma in tuna ba ni cin amanar Allah sabad da tantiri,
Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi Na Abu Shayi dai ɗa ne,
Sun ka ce ba haka mun ka so ba ɗan yaro,
Ai mun san ɗa ne tun da an ka haihe shi,
Ba mu labari in akwai gidan kirki,
Nic ce i gaskiyak ka dattijo,
Mutun kau ba za ya kai ɗiyatai ba gidan da ba abin kirki,
Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi,
Sai ɗiyad dattiɓai kaɗai ka amre Shayaya ɗan gidan Labbo,
Tun da ko wa a amre shi ita ka cishe shi,
Ta biya kuɗɗin garin karen kyarson,
Sannan ta yi mai abin ruhwa koren
Kana ta koma ta yi dabbarin abin ɗauri.
Dattijo yat tashi
Yab buge riga

Yay yi cikin zaure
Yac ce ma ɗiyatai
Ga tciyakki nan samna
Ke da kin ka zaɓo shi
Ashe ta ɗauki ba na kowa ba.

A ɗiyan waƙar da ke sama na waɗanda suke a matsayin baitin farko an samu yi wa Kassu tambaya a kan an ba shi amana ya faɗa gaskiyar labarin wane ne Shayaya ɗan gidan Labbo don wasu mata sun riga sun walwale baikonsu kuma sun ce Shayaya sai ya yi rankonai, don su aure suke so su yi, don haka a faɗa musu idan gidan kirki Shayaya ya fito. A nan Kassu ya nuna gaskiya sun ɗaure shi don amana wuya gare ta. Kassu ya nuna da su nemi wani su tambaya shi don Shayaya ɗan'uwansa ne, ba yadda za a yi ya yi shaidun sa, kuma ma shari'a ta tabbatar da haka. A ɗiyan waƙar da suke a matsayin baiti na biyu, an dage da sai Kassu ya ba da labarin da aka tambaye shi na Shayaya. A nan Kassu cikin hikima irin tasa ya yi tunanin yadda zai amsa tambayoyin don ba ya so ya ci amanar da aka ɗora masa, saboda wanda ake son ya ba da labarinsa tantiri ne.
Daga nan sai ya fara bayani cikin hikima, inda ya nuna wannan da ake tambayar labarinsa ɗa ne ba bawa ba, sai masu tambayar suka nuna ai sun san da ɗa ne tunda haihuwarsa aka yi, su muradinsu shi ne, su san halayyar gidansu ta kirki ce ko akasin haka ce. Kassu ya ci gaba da bayani cewa lallai babu dattijon da ba ya son ya kai ɗiyarsa gidan kirki, amma su sani wanda suke son su kai ɗiyarsu gidansa to lallai ba ya iya ciyar da iyali sai dai a cishe shi, sannan bayan an cishe shi akwai sauran buƙatocin da dole sai an yi masa. To a nan sai dattijo ya ce wa 'yarsa ga tsiyar da ta kwaso nan shi ba ruwansa don ita ba ta ma san wanda ta kawo ba.
Abin lura a nan ga ɗiyan waƙoƙin da aka ɗan yi tsokaci kaɗan a kansu shi ne, Kassu ya san matsayin amana a Musulunci don haka ya ƙi yarda ya yi ƙarya ga tambayar da aka yi masa don kawai ya kaucewa cin amana. To wai mi ake nufi da amana kuma ya matsayinta yake a Musulunci?

Amana a Musulunci wata babbar alƙibla ce da ke daga cikin muhimman halaye da ginshiƙan kyawawan ɗabi'u a Musulunci. Kalmar amana na nufin nauyin da aka ɗora wa mutum wanda dole ne ya kula da shi cikin gaskiya da amincewa da adalci. A jumla ce kuma, amana tana nufin kiyaye duk wani nauyi da aka ɗora wa mutum na dukiya ko aiki ko sirri iko ko shugabanci da yin aiki da gaskiya da bin shari'a a dukkan al'amurra na yau da kullum da riƙo da alƙawari da sauran mu'amalolin rayuwa baki ɗaya.

Allah Maɗaukakin Sarki na cewa "Lalle Allah yana umartar ku da ku mayar da amanoni zuwa ga masu su" (Alƙur'an, Sura ta 4 aya ta 58). Wannan aya ta nuna cewa amincin amana yana daga cikin manyan umarnin Allah ga bayinsa. Amana abu ce da sammai bakwai da ƙassai bakwai da duwatsu suka kasa ɗaukarta saboda nauyinta, amma shi mutum da yake ɗan tarar aradu da faɗi ne sai ya ce ya ji ya gani zai iya ɗauka. Allah Maɗaukakin Sarki na cewa "Lalle ne mun gitta amana ga sammai da ƙassai da duwatsu, sai suka ji tsoro daga gare ta, kuma mutum ya ɗauke ta, lalle shi mutum ya kasance mai yawan zalunci mai yawan jahilci (Alƙur'an, Sura ta 33 aya ta 72). Wannan aya ta bayyana cewa amana babban nauyi ne da sammai da ƙassai suka ƙi ɗauka, amma mutum ya ɗauke ta. Tana nuni da girman nauyin amana da kuma irin halin da mutum ke shiga idan bai kiyaye ta ba. Maganganu da yawa sun tuzgo a sunnar Manzon Allah (SAW), wanda wannan ba muhallin ambatonsu ne baki ɗaya ba, kaɗan daga ciki akwai cewa, babu imani

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

ga wanda ba shi da amana. Hakayana daga cikin alamomin da ake gane munafuki, idan aka danƙa masa amana ya yi ha'inci wato ya ci amanar.

Akwai ire-iren amanoni a Musulunci kamar amana ta dukiya wadda ita ce– danƙa wa mutum abu irin kuɗi ko kaya ko dabbobi don ya kiyaye su. Akwai amana ta aiki ko shugabanci. Akwai amana ta sirri wadda mutum zai bayyana maka abu ya ce ka da ka faɗawa kowa da dai sauransu da yawa.

## 3.0 Sakamakon Bincike

A wannan binciken da aka gabatar an gano cewa waƙoƙin Makaɗa Kassu Zurmi waƙoƙi ne da suka tara abubuwa da yawa da suka shafi rayuwa baki ɗaya. Waƙoƙi ne da ke ɗauke da karantarwa da ilmantarwa da nishaɗantarwa. Nazarin ya gano cewa duk da kasancewar Kassu Zurmi bai yi zurfaffen karatun addini ba, amma tabbas ya fahimci wasu hukunce-hukunce addini masu ƙarfi, musamman sallah da azumi da zakka. Haka binciken ya gano cewa duk da kasancewar waƙoƙin Kassu waƙoƙi ne na maza da suka shafi tauri da sata da farauta da makamantansu, waɗanda mutane ke yi wa kallon miyagun ɗabi'u ne da ba su da wata fa'ida ta a zo a gani kuma saurarensu na iya canja halayya mai kyau zuwa maras kyau, to amma fa akwai fa'idoji masu tarin yawa a ciki da suka shafi Musulunci da aka tsinta a ciki a dalilin tasirantuwar da addinin Musulunci ya yi a rayuwar makaɗin.

## 4.0 Kammalawa

Kamar yadda bayanai suka gabata na wannan bincike za a ga nazarin ya yi duba ne a kan gurbin Musulunci a wasu waƙoƙi biyu daga cikin waƙoƙin da Kassu Zurmi ya yi. an zaɓi 'Waƙar Iro Shayi ɗan gidan Labbo' da 'Waƙar Malam Sanda ɗan Ruhwa'i', wannan maƙala ta yi tsokaci kaɗan kan hanyoyin da aka bi wajen tara bayanai, sannan ta zo da taƙaitaccen tarihin Kassu Zurmi da matsakaicin bayani kan fitilun kalmomin bincike. Daga nan aka shiga bayani kan gundarin nazarin da aka yi, inda aka yi bayanin wasu ɗiyan waƙoƙin da Kassu ya ambata, ya gina su ne saboda tasirin da Musulunci ya yi a rayuwarsa. An rufe maƙalar da faɗin sakamakon da binciken ya gano da manazarta.

## Manazarta


Abrams, M. H. and Harpham, G. G. (2012). A Glossary of Literary Terms (10th ed). U S A: Wadsworth Engaged Learning.

Albarbahari, A. H. A. (2013). *Sharhul Sunnah.* Cairo-Egypt: Daral Hadyu Muhammady.

Bargery, G.P. (1993) *A Hausa English Dictionary and English Hausa Vocabulary.* Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Buhari, M. I. (2019). *Sahih Albuhari.* (ed) Online at Sunnah.com

Bunza, A.M. (2014). *In Baka san Gari ba Saurari Daka: Muryar Nazari Cikin Tafashen Gambo.* Cairo: Elkods Printing House.

Funtua, A.I. (2015). Nazari a Kan Waƙoƙin Makaɗan Baka na Hausa a Jihar Katsina Daga 1978 Zuwa 2012. Kundin Digiri na Uku (Ph.D Thesis) . Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero, Kano.

Ɗangambo, A. (1984). *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kano: Maɗaba'ar Kamfanin 'Triumph' Gidan Sa'adu Zungur.

Gusau, S.M. (1988). Waƙoƙin Makaɗan fada: Sigoginsu da Yanaye-yanayensu. Kundin Digiri na uku (Ph. D Thesis). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Magaji, A. (2016). Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa. Ibadan: Specrum Books Limited.

Gummi, A. M. (1979). Fassarar *Al-Kur'ani Mai Girma.* Madina: Rabiɗatul Alam el-Islam.

Gusau, S.M. (1995, 2003). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Sa'id, B. (2006). *Kamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Garba, S. (2020). 'Ƙurɓushin Musulunci a Tunanin Bahaushe: Tsokaci daga Tatsuniyar Ruwan Bagaja'. A cikin Ɗunɗaye Journal of Hausa Studies. Mujallar Nazarin Hausa. Vol. 2 No. 3. Department of Nigerian Languages. Sokoto: Usmanu Danfodiyo University.